Babu imani ga wanda ba shi da amana, kuma babu Addini ga wanda ba shi da alƙawari

Daga Anas ɗan Malik - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - bai taɓayi mana wata huɗuba ba sai ya ce: «Babu imani ga wanda ba shi da amana, kuma babu Addini ga wanda ba shi da alƙawari».

[Hasan ne da wani Sanadin] [Ahmad ne ya rawaito shi]

Anas ɗan malik - Allah Ya yarda da shi - yana bada labarin cewa da wahala Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi huɗuba ko ya yi wa'azi sai ya ambaci al'amura biyu: Na farko: Babu imani cikakke ga wanda a ransa akwai ha'inci ga wani mutum a cikin dukiyarsa ko ransa ko kuma iyalansa. Na biyu: Babu Addini cikakke ga wanda yake ha'intar alƙawurra kuma yake warwaresu.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/66251